**KNJ PHASE III**

**EPISODE 20**

**Characters**

*Danjuma*

*Tina*

*Alhaji Bature*

*Hindatu*

*Kande*

*Husseini*

**SCENE 1**

*Danjuma's House*

1. **SFX**: <u>**SOUND OF DOOR OPENING AND SLAMMING SAINT**</u>.
2. **SFX:** <u>**SOUND OF METAL POTS**</u>
3. **DANJUMA**: (**OFF. MIC. CALLING OUT, ANGRILY**) Tina!
4. **SFX**: <u>**SOUND OF DOOR OPENING**</u>
5. **TINA**: Ay Yaya Danjuma, sannu da zuwa. Ina sharshre kicin kenan kuma……….
6. **DANJUMA**: (**CUTS IN ANGRILY**) me ya faru yau da rana?

7. **TINA**: (**INNOCENTLY**) yau da rana? Yaya Danjuma, kamar yaya? Me kake nufi?

8. **DANJUMA**: (ANGRY) ina nufin kamar yadda na tambaye ki. Me ya faru a gidan nan yau da rana? Me ki ka gayawa Hannah?

9. **TINA**: (**GIGGLES NERVOUSLY**) Ah Yaya Danjuma, ina ganin baka cikin yanayi mai kyau. Watakila don kana jin yunwa ne. a duk lokacin da kawu na yake jin yunwa……..

10. **DANJUMA**: Kalli Tina, abinci ba matsala na bane yanzu ki amsa tambayata kawai. Me ya faru a tsakaninku da Hannah yau da rana?

11. **TINA**: Kalli Yaya Danjuma, watakila kana iya gayamun abin da kake Magana a kai.

12. **DANJUMA**: (**BLURSTLY OUT**) Hannah tace kin gayamata muna ma'amala a asirce.

13. **TINA**: (**PRETENDS SHOCK**) Ah!!! Mene? Har abada!

14. **DANJUMA**: Gaskiya! Tace ta dawo gida ta taradda mu a tare kuma a lokacin da nake barci ki ka gaya mata.

15. **TINA**: Kalli Danjuma, zan iya rantsewa da duk abinda ka kawo ban gaya mata ba. Saboda me zan gaya mata haka.

16. **DANJUMA**: Kina nufin karya take yi?

17. **TINA**: (**SNIFFLES**)

18. **DANJUMA**: Ya isa, Tina. Shike nan ki daina kuka.

19. **TINA**: (**SNIFFLES**)

20. **DANJUMA**: Ban san dalilin da Hannah zatayi wannan kazafi bayan tasan ina sonta kwarai.

21. **TINA**: Ah Yaya Danjuma, ka san matsoraciya ce. Kullum ta kan tambaye ni akan das u ke offishin ka.

22. **DANJUMA**: (**INTERRUPTS**) Kariya? Amma Tina, bata farga ba cewa bana iya kallon ko wace mace, ita kadai kawai nakeso.

23. **TINA**: (**SUCKS TEETH**) tan a kishinane, ina tsammanin tana jin nib a tsararta bace.

24. **DANJUMA**: Wannan bai da ma'ana, Tina.

25. **TINA**: Baka tuna yadda hankalinta ya tashi idan taga ina aikace-aikace a gidan ba? Tana tunanin kokari nakeyi in kwace mata kai.

26. **DANJUMA**: Hmm amma Tina, ina tunanin na tabbata abinda take fada gaskiyane. Inda bah aka ba, yaya har zata gaya wa mahaifiyarta, idan batana da tabbaci gaskiya bane?

27. **TINA**: Hmm Danjuma: kayi bincike kwarai kuwa a kanta kafin ka aureta?

28. **DANJUMA**: (**CONFUSED**) saboda me kika tambaya……

29. **TINA**: (**CUTS IN**) Ah babu wanda ya tabe gaya maka cewa a kwai tarihin cutar hauka a bangaren mata a cikin danginsu?

30. **DANJUMA**: (**SHOCKED**) Hauka?

31. **TINA**: Kwarai! Ance kuma suna faraway ne idan mace nada ciki. Na tabbata dalilin da yasa Hannah take kirkiro wa'annan labaran.

32. **DANJUMA**: (**ANGRILY**) Yanzu kina nufin matata mahaukaciyace, Tina, eh? Kina ganin zamanki anan bai yi illa ba kuwa?

33. **TINA**: (**BACK TRACKING**) Kayi hakuri: Yaya Danjuma. Bani da niyar saba maka. Don allah kar ranka y abaci.

34. **DANJUMA**: (**FLATLY**) Kalli Tina, ina jin zai fi kyau ki tafi, bai kamata ba ace nida ke muna cikin gidan nan mu biyu kawai, balle ma ga zargin da Hannah ta keyi.

35. **TINA**: Ah amma wannan ba adalci bane. Ba muyi wani abu dab a dai-dai ba.

36. **DANJUMA**: Tina, ina ganin ya kamata ki tafi, zan iya baki kudi ki kwana a otel da kuma kudin motar kid a safe gobe.

37. **TINA**: A'a Yaya Danjuma, wa zai kula da kai idan na tafi? Ina da kawar d azan zauna da ita. Ta haka zan rinka zuwa ina yi maka girki da kuma shara.

38. **DANJUMA**: Nagode, Tina. Nayi murna da wannan tayi, amma babu dalilinki na yin haka.

39. **MUSIC**: <u>**BRIDGE MUSIC**</u>

**SCENE 2**

*Alhaji Bature's Residence*

40. **SFX**: <u>**SOUND OF CHILDREN PLAYING**</u>

41. **SFX**: <u>**SOUNDS OF CROCKERY AND CLINNING CUTTERY**</u>.

42. **ALHAJI**: Hindatu, me nene a cikin flask din abincin nan?

43. **HINDATU**: Ah Alhaji, perpesu ne.

44. **ALHAJI**: (**IRRITATED**) wace irin shashashar amsace wannan? Menene "perpesu". Baza ki iya gaya mun wane irin perpesu bane? Ko na zama aljani ne yanzu?

45. **HINDATU**: Yi hakuri maigida, kayan ciki ne.

46. **SFX**: <u>**SOUND OF FOOD FLASK OPENING**</u>

47. **ALHAJI**: Hmmmm rufe shi! Baya kamshin sabo.

48. **HINDATU**: (**SURPRISED**) Amma bature nine da kaina na dafa shi yanzu.

49. **ALHAJI**: (**CUTS IN, ANGRILY**) Hindatu baki jinni bane? Nace bana so!

50. **SFX**: **<u>SOUNDS OF CROCKERY AND CLINKING CUTLERY</u>**

51. **SFX**: **<u>SOUNDS OF CHILDREN PLAYING INTENSIFIES ON MIC</u>**

52. **ALHAJI**: (**ANGRILY**) Hey, hey, hey! Me nene wannan?! Yi min shiru anan! Yaran banza! Babu dama in sami kwanciyar hankali kwata-kwata.

53. **SFX**: **<u>SOUNDS OF CHILDREN PLAYING MUTES</u>**

54. **ALHAJI**: Hindatu, wai baza ki iya sa yaran nan suyi shiru bane?

55. **HINDATU**: Haba Alhaji, kaifa kace idan ka shigo a barsu su rinka wasa a palo saboda ka rinka ganinsu.

56. **ALHAJI**: (**UPSET, CALLS OUT TO CHILDREN**) Ke! Dauki kannanki zuwa daki, ki kuma tabbata kinyi aikin gidanki.

58 **SFX**: **<u>SOUNDS OF DOOR OPENING AND CLOSING</u>**

59. **ALHAJI**: Dawo mun da perpesun.

60. **HINDATU**: (**TAKEN ABACK**) Amma Alhaji kace…..

61. **ALHAJI**: (**CUTS IN DEFENSIVELY**) Mene? Me ki kace?

62. **HINDATU**: Bakomai maigida, gashi.

63. **SFX**: **<u>SOUNDS OF CUTLERY CLINKING</u>**.

64. **HINDATU**: (**HESITANTLY**) Alhaji, ina bukatar wasu kudade domin saye-sayen yara.

65. **AL`HAJI**: Kuma wane saye-saye ne da baya karewa.

66. **HINDATU**: Toh Alhaji, duk kayan babban yaron mu sunyi masa kadan, kuma Saratu tana bukatar sababbin takalman makaranta.

67. **ALHAJI**: (**INTERRUPTS RUDELY**) Ki tura bukatunki ga mahaifin wannan yaran.

68. **HINDATU**: (**CONFUSED**) Ai maigida, shi yasa nake gaya maka bukatun yaran mu.

69. **ALHAJI**: Kalli Hindatu, bari in gaya miki yanzu, na gaji da daukar wa wani mutum nauyinsa.

70. **HINDATU**: (**WAILING**) Subhanallah (Alhamdulillah) Alhaji!

71. **ALHAJI**: Ahap (**EXPRESSION OF UNCONCERN**) ki dai yi tsakani da Allah. Na san cewa yaran nan ba nawa bane.

72. **HINDATU**: (**WAILING**) Wayoooo Alhaji! Me yasa Alhaji zai gaya mun haka? Heeee yoooo! Tawa ta kare! Waye zai gasganta wannan?

73. **MUSIC**: **BRIGDE MUSIC**

**SCENE 3**

*DANJUMA AND HANNAH'S RESIDENCE*

74. **SFX**: <u>**SOUND OF A DOOR BELL**</u>

75. **TINA**: (**ON MIC**) Na'am? Waye ne?

76. **KANDE**: (**CALLING OUT**) Maman Hannah ce.

77. **SFX**: <u>**SOUND OF DOOR OPENING**</u>

78. **TINA**: Ah anty Kande, kece/don Allah shigo

79. **KANDE**: (**UPSET**) Ke kuma, Tina me k eke yi anan? Ba kida kunya?

80. **TINA**: Anty Kande ……

81. **KANDE**: (**CUTS IN**) kada ki kirani anty Kande, Tina! So kin shawarta zama anan duk da yar'uwarki bata nan, duk da zargin da a ke yi miki?

82. **TINA**: Anty Kande, don Allah ki dakata! Ba wai ina zama a nan bane, na zo in taimakawa Danjuma girki da kuma shara ne.

83. **KANDE**: (**GRUNTS**) Mmmm. Toh tina. Ina Danjuma, shi nazo gani.

84. **TINA**: Bai dawo daga offis ba, yana yin aiki da yawa kwanakin nan Anty.

85. **KANDE**: Tina, zo mu zauna. Na yi kokari in ganki amma ba kya daukar waya ta.

86. **SFX**: <u>**FOOTSTEPS AND SOUND OF CHAIR DRAGGING ON THE FLOOR AS THEY SIT.**</u>

87. **TINA**: Anty Kande bah aka bane. An sace waya tane. Kuma na sha wuya sosai. Yanzu ina rabe da abokiyar aikina ne (SOBBING) Abin ba sauki.

88. **KANDE**: Kalli yarinyar nan, idan dai haka abin yake, me yasa baki neme nib a? niba Anty ki bace?

89. **TINA**: Haka ne, amma Anty Kande….

90. **KANDE**: Bugu da kari halin da kuke ciki da mijin yar'uwarki, akwai wannan zargi a kanki amma baza ki iya nema na a kan maganar ba.

91. **TINA**: Anty na san Hannah na zaune a wurinki shiyasa ban zoba. Ba na son in jawo rigima.

92. **KANDE**: O-ho Tina. Shi yasa ki ka gaya wa yar'uwarki cewa a kwai wani abu a tsakanin ki da mijinta?

93. **TINA**: (**WAILING**) Ah Anti Kande, ba gaskiya bane! Ban san dalilin da Hannah ta kirkiro wannan labara ba.

94. **KANDE**: Tina……

95. **TINA**: (**WAILING**) Mama! Mama!! Mama!!! Mama sabo da kin mutu, babu wanda zai kare yarki a yanzu.

96. **KANDE**: (**SHOCKED**) Ki kwantar da hankalinki, Tina.

97. **TINA**: (**GASPING FOR BREATH**) Ehhh! Mammmmaaaa!!! Mama, kalli halin da nake ciki!!!

98. **KANDE**: Toh fa! Tina. Babu damuwa, ki kwantar da hankalinki kada rashin lafiya ya kamaki.

99. **TINA**: (**WAILING**) Heh Mana! Don Allah ina kike? Hannah tana da mahaifiyarta da zata tsaya mata, me yasa ke bazaki goyi bayana ba?

100. **KANDE**: Tina! Nace ya isa. Kada ki dauke shi haka har yanzu ke yar'uawatace. Kwantar da hankalinki.

101. **TINA**: (**SNIFFLING**)

102. **KANDE**: Ban ma san wane labara zan yarda da shiba yata bata taba yimun karya ba……

103. **TINA**: (**RESUMES WAILING**) Watau nice makaryaciya? Saboda bani da uwa ko kuma mai kareni? Shi yasa nice makaryaciya?

104. **KANDE**: Kalli Tina, ban ce kece makaryaciya ba. Ina dai cikin tsaka mai wuya ne.

105. **MUSIC**: <u>**BRIDGE MUSIC**</u>

**SCENE 4**

*ALHAJI BATURE'S STORE*

106. **SFX**: **<u>SOUND OF A KNOCK ON THE DOOR</u>**

107. **HUSSEINI**: Alhaji Bature, salam alaikum

108. **ALHAJI**: (**GRUNTS**)

109. **HUSSEINI**: Salam alaikum, Alhaji

110. **ALHAJI**: Nace wa alaikum salam, Husseini.

111. **HUSSEINI**: (**LAUGHS NERVOUSLY**) Kayi hakuri yallabai, banji kaba! Ina wuni, Alhaji.

112. **ALHAJI**: Ina wuni

113. **HUSSEINI**: Ya iyali>

114. **ALHAJI**: Lafiya

115. **HUSSEINI**: Nazo in biya bash inane, Alhaji.

116. **ALHAJI**: Toh, nawa ka kawo?

117. **HUSSEINI**: Naira dubu biyar.

118. **ALHAJI**: (**SUCKS TEETH**)

119. **HUSSEINI**: Alhaji, alkawarin da mukayi kenan.

120. **ALHAJI**: (**COLDLY**) Kawo. (**PAUSE**) Kalli wannan kudin, Husseini. Daga mahauci ka karbo su ne? ina ka ke so in ajiye wannan kudi masu datti?

121. **HUSSEINI**: Alhaji ya dai kamar ba kai ba.

122. **ALHAJI**: Duniyarce gaba daya ta kini.

123. **HUSSEINI**: Alhaji ina ganin ya kamata in dawo wani lokaci, domin naga kamar ba zamu iya tattauna kasuwanci yanzu ba.

124. **ALHAJI**: Idan ka dawo anjima zaka gaya mun Hassan ya janye daga takara?

125. **HUSSEINI**: ERM……..

126. **ALHAJI**: (**RUDELY**) Ina Magana da kaina ne ko ina magana da kai, Husseini?

127. **HUSSEINI**: Toh Alhaji, idan nace abin da zai kawo ni kenan, nayi maka karya.

128. **ALHAJI**: A takaice dai yaki yanye wa ken an.

129. **HUSSEIMI**: Alhaji nayi kokarin in ja hankalinsa, amma ya tubure.

130. **ALHAJI**: Duk wannam labarine, kokarinka ya zama a iska, wace hujja kuma zaka bani?

131. **HUSSEINI**: Alhaji, in gaya maka gaskiya babu wani abu d azan iya a yanzu, nayi kokari amma dan uwana ya turje. Don Allah Alhaji……

132. **ALHAJI**: (**CUTS IN, COLDLY**) Toh, tunda haka ne Husseini, babu abinda zan kara yi maka.

133. **MUSIC**: <u>**BRIDGE UP AND FADE UP AND UNDER**</u>